# Mafi alherinku shi ne wanda ya koyi Alkur’ani kuma ya koyar da shi

Daga Usman Allah Ya yarda da shi daga Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi ya ce: "Mafi alherinku shi ne wanda ya koyi Alkur’ani kuma ya koyar da shi".
[صحيح] [رواه البخاري]

Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana ba da labarin mafi falalar Musulmai, wanda kuma yake ƙololuwar daraja a wurin Allah shi ne, wanda ya koyi Alƙur’ani, karatun da hadda da rerawa da fahimta da Tafsir. Ya kuma sanar da wani abin da yake wurinsa na iliman Alkur’ani (Ulumul Qur’an) tare da aiki da shi.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee